# SŨRATUL 'ÃDIYÃT سُورَةُ العَادِيَاتِ

Tana karantar da yadda ake yin hari da lõkacin da ake yaƙin kãfirai, da dalilin da ya sa a yãƙe su.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Ina rantsuwa da dawãki mãsu gudu suna fitar da kũkan ciki.

*2.* Mãsu ƙyasta wuta (da kõfatansu a kan duwatsu) ƙyastawa.

*3.* Sa'an nan mãsu yin hari a lokacin asuba,

*4.* Sai su motsar da ƙũra game da shi.

*5.* Sai su shiga, game da ita (ƙũrar), a tsakãnin jama'ar maƙiya.

*6.* Lalle ne mutum mai tsananin butulci ne ga Ubangijinsa.

*7.* Lalle ne shi mai shaida ne a kan laifinsa da haka.

*8.* Kuma lalle ne ga dũkiya shi mai tsananin so ne.

*9.* Shin, bã ya da sanin lõkacin da aka tõne abin da yake cikin kaburbura,

*10.* Aka bayyana abin da ke cikin zukata,

*11.* Lalle ne Ubangijinsu, game da su, a ranar nan, Mai ƙididdigewa ne ?

وَٱلْعَٰدِيَٰتِ ضَبْحًا ۝١

فَٱلْمُورِيَٰتِ قَدْحًا ۝٢

فَٱلْمُغِيرَٰتِ صُبْحًا ۝٣

فَأَثَرْنَ بِهِۦ نَقْعًا ۝٤

فَوَسَطْنَ بِهِۦ جَمْعًا ۝٥

إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لِرَبِّهِۦ لَكَنُودٌ ۝٦

وَإِنَّهُۥ عَلَىٰ ذَٰلِكَ لَشَهِيدٌ ۝٧

وَإِنَّهُۥ لِحُبِّ ٱلْخَيْرِ لَشَدِيدٌ ۝٨

۞ أَفَلَا يَعْلَمُ إِذَا بُعْثِرَ مَا فِى ٱلْقُبُورِ ۝٩

وَحُصِّلَ مَا فِى ٱلصُّدُورِ ۝١٠

إِنَّ رَبَّهُم بِهِمْ يَوْمَئِذٍ لَّخَبِيرٌۢ ۝١١